# Littafi mai Tsarki na yara

## Ke gabatar da

# Basamariye Mai Kirki



**Wanda ya Rubuta: Edward Hughes**

**Mai Zane: M. Maillot; Lazarus**
**Alastair Paterson**

**Mai niyyan daukan nauyi: Ruth Klassen; Sarah S.**

**Fassarawa: Bible Society Nigeria**

**Wanda ya Wallafa: Bible for Children**
**www.M1914.org**

**©2024 Bible for Children, Inc.**
**Zaku iya kofan wanna labarin ku wallafa idan har ba zaku sayar da shi.**





**"Mallam! Mene ne ya zama lallai sai na yi kafin in sami rai madawwami?" Wanda ya yi wannan tambaya Loya ne, kuma kokarinsa shi ne ya rinjaye Yesu. "Mene ne dokan Allah ya ce?" Yesu ya amsa masa.**


"Kaunace Allah
da makwabcin
ka," mutumin ya
ce. "Amma wane
ne makwabci na?"
ya tambaya.
3


Domin ya amsa tambayar mutumin, Yesu ya gaya
masa wani labari game da mai tafiya a hanya daga
Urushalima zuwa Yeriko.
Mutumin barayi sun
kai masa hari.
4


Barayin suka sata kome da komen da yake da
shi, har suka kwace rigunansa. Suka kuma ji
masa rauni sosai, suka bar shi bakin mutuwa
a bakin hanyan.
5


Sai ga wani firist ya iso wurin. Babu
shakka zai taimaki shi mai raunin.
A'a! Sa'ad da ya gan
shi kuma jini yana
sauka, sai ya
bi gefe daya na hanyar ya tafi.
6


Ba a dadde ba sai ga motsin kafa na wani yana zuwa.
Shi mutumin Lawi ne – mutumin da yake taimakon
firist a aikin haikali. Sai ya je ya dubi
mutmin da aka ji masa ciwo, sai shi
ma ya bi gefe bai
taimaka ba sai ya tafi.
7


A karshe sai ga Basamariye ya iso. Yahudawa
sun ki jinin Samariyawa. Mutanen da suke
sauraron labarin Yesu ba za su yi zatto
cewa Basamariye ne zai zama
gwani ba.
Amma shi ne
gwanin.
Basamariyen ya lura, ya tsaya
domin ya ba da taimako.
8


Basamariyen ya durkusa, a hankali ya shafa magani da bandaji a kan ciwon bakon nan. Sa'an nan ya taimake mai raunin nan ya hau kan jakinsa.
9


A wani gidan hutu a bakin hanya, Basamariyen ya lura da mutumin a daren har gari ya waye.
10


Washegari sai ya biya kudin da ake bukata domin a lura da matafiyin har sai ya warke kuma.
11


Labarin ya kare. Yesu ya tambaye su, "Wa ne ne makwabcin mutumin da ya ji rauni?"
12


Wannan Loya ya amsa, "Makwabcinsa shi ne Basamariyen nan wanda ya nuna tausayi."
13


"Jeka, kai ma ka yi haka," Yesu ya ce. Makwabci shi ne kowane mutum wanda yake da bukata. Za mu iya nuna kauna ta wurin taimaka wa mutane masu bukata. Wannan yana faranta wa Allah rai.
14

**Basamariye Mai Kirki**

**Tahiri da ga maganar Allah, littafi mai Tsarki**

**a na samu a**

**Luka 10**

**“Shigowar maganar ka yana baduar kawo haske.” Zabura 119:130**






46 60



**Wanan tahiri daga littafi mai-tsarki na mana bayanin Allah mu wanda ya halicce mu wanda yake son mu san shi.**

**Allah ya san da cewa mun yi abubuwan da ba su da kyau, wanda yake kira zunubi. Sakamakon zunubi mutuwa ne, amma Allah ya na kaunan mu sosai. Ya aiko da Ɗansa Yesu, ya mutu a kan giciye ya sha wahala domin zunuban mu. Kuma sai Yesu ya tashi daga matattu ya koma gida a sama. Idan ka bada gaskiya ga Yesu. Ka roƙeshi gafaran zunuban ka, zai yafe. Kuma zai zo ya zauna a cikin zuciyan ka kaima kuma zaka zauna a zuciyar shi har abada.**

**Idan ka yadda da wannan gaskiya ne, Ka cewa Allah:**
**Ya Yesu, na bada gaskiya kai Allah ne, ka kuma zamu mutum don ka mutu domin zunubi na, kuma yanzu ka tashi. Ina roƙon ka, ka shiga cikin zuciya na kuma ka yafe min zunubai na, Domin in samu sabon rai yanzu, kuma wata rana in zauna tare da kai har abada. Ka taimake ni in yi maka biyayya kuma in yi rayuwan da zai gamshe ka a matsayin ɗan ka. Amin.**

**Ka karanta littafi mai-tsarki kuma ka yi magana da Allah a kulla yaumin. Yahaya 3:16**